

# Iya Gani Iya Kyalewa

Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 3

Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Iya Gani Iya Kyalewa
Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN
Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright:  SIL International 2009




Akwai wani Ɗanfulani.
Yana shiga gari  cin kasuwa.
Ga dutse kan maciji.



A kan hanya Ɗanfulani ya ga maciji.
Ga babban dutse kan maciji.





Maciji ya roƙi Ɗanfulani.
Ya na son a cire dutse.
Ɗanfulani ya yi shakkar cirewa.




Maciji ya ce babu  damuwa.
Maciji ya ce Ɗanfulani ya masa rana.
Shi kuma ba zai masa dare ba.




Ɗanfulani ya ɗaga dutse.
Maciji ya fita ƙasan dutse.
Sai maciji ya ɗaga kai.
Zai ciji Ɗanfulani.



Ɗanfulani ya ce na yi maka rana.
Yanzu kana son ka yi mani dare.



Can sai ga kare ya zo.
Ɗanfulani ya mai da zance.
Kare ya ce ga mafita.





Kare ya ce maciji ya kwanta.
Ɗanfulani ya mayar da dutse.
Kare ya ce iya gani iya ƙyalewa.

ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK